**JUMHURIYYAR MISRA TA LARABAWA** **26 Rajab, 1444**

**MA'AIKATAR ADDININ MUSULUNCI** **17 Fabrairu, 2023**

(١)

# MU'UJIZAR ISRA'I DA MI'IRAJI DA KARFIN IKON ALLAH

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **(Allah ya tsarkaka ga barin duk wani abu da bai dace da shi ba, shi ne wanda ya yi tafiyar dare da bawansa Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) a cikin wani yanki na dare daga Masallacin Harami na Makka, zuwa Masallacin al- Aƙsa da yake a garin Baitul Maƙdisi, wanda Allah ya yi wa mazauna wurin albarka a cikin abincinsu; saboda mu nuna masa wasu daga cikin ayoyinmu da suke ɗauke da cikakkun hujjoji, kuma gamsassu akan kaɗaitakarmu da girman ikonmu, lallai Allah shi kaɗai shi ne mai yawan ji da gani)** [al- Isra'i: 1]. Ina shaida cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina kuma shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammad bawan Allah ne kuma Manzonsa, Ya Allah Ubangiji ka ƙara masa tsira da aminci da albarka, shi da alayensa da sahabbansa, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, Bayan haka:

Lallai tafiyar Isra'i da Mi'iraji wani babban girmamawa da karamawa ne da Allah ya yi wa Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), sannan kuma ɗauke masa damuwa, da yaye masa baƙin- ciki ne, bayan ya jure wa cutarwar da mutanensa suka yi masa, ya kuma jajirce duk irin yanda suka juya wa kiransa da cikakken saƙon da ya zo da shi baya, bayan kuma ya rabu da masoyiyarsa da take ɗebe- masa- kewa, ya kuma yi ban- kwana da jajirtaccen Baffansa mai kwarjini, sai Allah mai girma da ɗaukaka ya keɓance shi da wannan babbar mu'ujiza, inda Allah Maɗaukakin Sarki ya nannaɗe wa Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) tazarar zamani, da na wuri; saboda ya nuna masa haƙiƙanin gaibi, da sirrorin halitta cikin cikakken ikonsa mai girma da ɗaukaka da ba shi da iyaka, hankali ma ba ya iya hararo shi, kaman yanda Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: **(Lallai ya wasu manyan ayoyin Ubangijinsa mai girma)** [an- Najmi: 18].

Duk wanda yake yi wa wannan babbar mu'ujiza ta Ubangiji kallo na lura da tsanaki, zai ga cewa tana cike ne da izina gami da darussa, farkon abin da za mu iya gani shi ne: **Darasin yaye damuwa bayan tsanani**, da kuma irin yanda Allah mai girma a koda yaushe yake tare da bayinsa muminai, da kuma wajibcin yin haƙuri, da rashin ɗebe- ƙauna, "komin runtsi da tsananin, duk abin da ya yi zafi", to kuwa zai yi sanyi, "duk abin da ya ƙuntata zai yi yalwa

ya faɗaɗa", duk wanda yake tare da Allah, to kuwa Allah yana tare da shi, babu wani al'amari da ba al'amarin Allah ba ne, haka ma babu wani hukunci da ba hukuncinsa ba ne, dukan halittu gaba ɗaya suna hannunsa ne, babu kuma yanda za a yi tsanani ɗaya ya rinjayi sauƙi guda biyu, Allah mai girmama da ɗaukaka yana cewa: **(Kuma lallai kowace wahala tana tare da sauƙi, da ma can a cikin kowace wahala akwai saaƙi)** [as- Sharh: 5 -6].

A cikin darussan da take ɗauke da su, akwai: **nuna daraja da ɗaukakar yi wa Allah mai girma da buwaya bauta**, inda Allah mai girma da ɗaukaka ya sifanta Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) da wannan sifa ta bauta a lokacin da yake matakin girmamawa da karramawa a gare shi, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Allah ya tsarkaka ga barin duk wani abu da bai dace da shi ba, shi ne wanda ya yi tafiyar dare da bawansa Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) a cikin wani yanki na dare..)** [al- Isra'i: 1], haka ma Allah mai girma yana cewa: **(Sai kuwa ya yi wa bawansa wahayin abin da ya so ya yi masa wahayinsa)** [an- Najmi: 10].

Haka ma a cikin darussan akwai: **fito da matsayi da muƙamin Masallacin Harami da Masallacin al- Aƙsa**, Allah mai girma yana cewa: **(Allah ya tsarkaka ga barin duk wani abu da bai dace da shi ba, shi ne wanda ya yi tafiyar dare da bawansa Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) a cikin wani yanki na dare daga Masallacin Harami na Makka, zuwa Masallacin al- Aƙsa da yake a garin Baitul Maƙdisi, wanda Allah ya yi wa mazauna wurin albarka a cikin abincinsu; saboda mu nuna masa wasu daga cikin ayoyinmu da suke ɗauke da cikakkun hujjoji, kuma gamsassu akan kaɗaitakarmu da girman ikonmu, lallai Allah shi kaɗai shi ne mai yawan ji da gani)** [al- Isra'i: 1], a cikin wani yanayi mai girma, da ya haɗe tsakanin Masallacin Harami da Masallacin al- Aƙsa; saboda wannan dangataka da take a tsakaninsu ta cigaba da zama a cikin hankula, da zukatan Musulmai har zuwa lokacin da Allah mai girma da buwaya zai gaje ƙasa da abubuwan da suke a kanta, daga Masallacin Harami ne Isra'in Sayyiduna RasullulLahi (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya fara, zuwa Masallacin al- Aƙsa, daga nan ne kuma Mi'irajinsa (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya fara zuwa sammai, har zuwa magaryar tuƙewa.

A cikin waɗannan darussa da izina akwai: **Bayanin ƙarfi, da girman ikon Allah Ubangiji, da kuma irin yanda Allah mai girma da buwaya ya karrama Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) da manyan ayoyi**, inda shi

kansa Isra'i da Mi'irajinsu sun kasance ne a dare ɗaya, haka ma Allah mai girma da ɗaukaka ya hore wa Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) Buraƙa; domin ta yi jigilar ɗaukansa a wannan tafiya mai albarka, ya kuma karrama shi da haɗuwa da Annabawa da Manzanni, inda Allah ya raya su; domin Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya yi masu limanci, su yi sallah a bayansa a Masallacin al- Aƙsa, ya kuma haɗu da waɗanda Allah ya ƙaddara masa ya haɗu da su a sammai maɗaukaka, suka yi maraba da shi, suka kuma yi masa addu'o'in alhairi; duka wannan wani nuni ne da yake tabbatar da cewa lallai ɗaukacin Annabawa da Manzanni (Masu tsira da aminci) mutane ne da suka zo da saƙo guda ɗaya a cikin asalin addini da imani, da kyawawan ɗabi'u, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Annabawa 'ya'yan uba ɗaya ne, addininsu ɗaya ne, iyayensu mata ne suka sha bamban)**.

A cikin darussan ma akwai: **bayani game da matsayi da muhimmancin sallah a rayuwar Musulmi**, lallai Allah mai girma da buwaya ya ƙaddara cewa ita ce kawai ya farlanta wa al'ummar Annabi Muhammadu a wannan dare mai albarka, a sama ba tare da wani tsani ba; wannan yana nuna cewa sallah ita ce mi'irajin muminai zuwa ga Ubangijin talikai, tana kyautata ɗabi'unsu, tana kuma ɗaukaka zukatansu, albarkacinta ne kuma rayukansu suke samun daraja, Allah mai girma yana cewa: **(Ka karanta masu abin da aka yi maka wahayi daga cikin Alƙur'ani, ka kuma tsayar da sallah; domin lallai sallah tana hana alfasha da abubuwan ƙi, lallai zikirin Allah shi ne abin da ya fi komai, Allah yana da cikakkiyar masaniya akan abin da kuke aikatawa)** [al-Ankabut: 45].

***

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga cikamakin Annabawa da Manzanni, shugabanmu Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Lallai bayanin da yake nuni zuwa ga riƙo da Asbab a fili yake, yana cikin muhimman darussan wannan tafiya mai albarka, kuma lallai hakan ba kishiya ne na dogaro da Allah mai girma da buwaya ba, hasali ma hakan ne ingantaccen mabuɗin ƙofar dogaro da Allah, lallai Allah Maɗaukakin Sarki yana da cikakken ikon ya yi wannan tafiya da Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), ba ta hanyar kowane irin tsani ba, ba shi ne ya ce: **(Da ma**

**can shi al'amarinsa idan ya so wani abu cewa yake da shi: kasance, nan take kuma sai ya kasance)** [Yasin: 82] ba, amma duk da haka sai ya hore wa Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) Buraƙa, domin ta zama ita ce hanya, da sila da za ta ɗauke shi a wannan tafiya, lokacin da Annabi (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya isa Baitul Maƙdisi kuma ya ɗaure wannan Buraƙa da Allah Maɗaukakin Sarki ya hore masa; saboda ya karantar da al'ummansa yanda za su rinƙa yin riƙo da Asbab, sai ya ce: **(Sai na ɗaure ta da maɗaurin da Annabawa suke ɗaurewa)**, haka ma lokacin da wani Balaraben ƙauye ya tambaye shi game da taguwarsa ya ce: Ya Manzon Allah, shin in ɗaure ta ne, sannan in dogara da Allah, ko kuwa in sake ta ne, sannan in dogara da Allah? Sai ya ce: **(Ka ɗaure ta, sannan ka dogara da Allah).**

**Ya Allah Ubangiji ka kare masa ƙasarmu, ka ɗaukaka darajarta a cikin ƙasashe.**